

# Little Ant’s Big Plan

Candice Dingwall Steven McKimmie Telri Stoop



Karamar Turuwa na sha'awar karatu. A kan yi wa Karamar Turuwa ba'a.

"Tururuwa ba su karatu. Dole ne tururuwa su ci abinci. Tururuwai na tara abincin da suke buƙata. ”





Karamar Turuwa za ta yi karatu a duk tsawon wuni, za ta yi karatu, ta yi takaratu har wunin ya kare.
Sauran tururuwan kuma sun ɗauki abin da suka iske don adanawa saboda a ƙarƙashin ƙasa.



Mahaifiyarta da mahaifinta sun yi matukar fushi, kuma Karamar Tururuwa ba tamji daɗi ba ko kadan.




A cikin kakar zubar ganyaye kasa, dole ne tururuwa su adana abinci a karkashin kasa.



Sarauniyar tana son abinci ta cika rumbu, saboda haka dole ne tururuwa suyi aiki tukuru.



Karamar Tururuwa ta fara ihu game da wurin da ta karanta.
"Gidan abinci ne muke bukata, wurin da mutane ke zuwa cin abinci.
"Ta faɗi haka a cikin littafan da na karanta. ”




Tururuwa suna tafiya ɗaya bayan ɗaya.
Suna tafiya a rana tsaka.






Kuma Karamar Tururuwa tace "Kai, akwai daya!"




Tururuwa suna tafiya daya bayan daya, dauke da burodin boga da burodin bun.






Da suka dawo Sarauniyar tayi murna.
Kantunan sun cika. Suna murna kamar mahaukata.



Mahaifiya da mahaifin Tururuwa sun rungume ta.



'Yar uwarta jaririya ta kama hannunta "Yanzu ina tsammanin na fahimta."

"Yadda kake son karanta littafi... Ya na sa ni son dubawa."

Babban Tsarin Karamar Tururuwa
Candice Dingwali,Steven Mckimmie da Telri Stoop
ne suka kirkiro

An yi lasisin wannan aikin a ƙarƙashin dokar Fasaha ta Kasa da kasa mai suna Creative Commons Attribution mai lamba 4.0. Wannan yana nufin cewa an yarda ka raba (kwafa da sake rarraba littafin ta kowace hanya ko tsari) da daidaita shi (garwaya shi, sake fasali, da ginawa kan littafin) akan kowane dalili, har ma da kasuwanci, idan dai za ka alakanta aikin da mai shi na asali, tare da nuna mahadar yanar gizon da za ta dauki mai karatu zuwa shafin littafin da ka yi amfani da shi, da kuma nuna canje-canje idan har an yi su a cikin aikin. Za ka iya yin hakan ta kowane hali mai ma'ana, amma ba ta kowace hanya da ta nuna cewa mai ba da izinin ya amince da kai ko amfanin ka ba.